**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.5 **Website:** www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Zuga A Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Asma'u Bello Balarabe**
Sashen Hausa, Kwalejin Ilimi Ta Shehu Shagari, Sakkwato

**Corresponding Author: Asma'u Bello Balarabe** bbalarabeasmau@gmail.com
**Lambar Waya : 08066183601**

**Tsakure**

*Zuga wata hanya ce da mawaƙa suke amfani da ita domin karsashi ko ƙwazo na abin da ake son ya aikata. Mawaƙa na amfani da wannan salo a cikin waƙa domin su wasa su kuma zuga wanda suke yi wa waƙa. Kasancewar Kassu makaɗin maza, dole ne ya yi amfani da salon zuga domin ya kwarzanta mutanensa. A wannan muƙala, an kawo ma'anar zuga da ire-iren waƙoƙin Kassu Zurmi waɗanda ake samun zuga a cikinsu. An kuma kawo misalan waƙoƙin Kassu Zurmi guda takwas tare da kawo inda aka sami zuga a cikinsu. Hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan muƙal shi ne ta hanyar saurarena waƙoƙi a MP da wayar salula da kuma littattafai da aka wallafa a kan Kassu Zurmi.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Zuga tana ɗaya daga cikin muhimman abubuwa a cikin waƙoƙin Kassu, domin tana ɗaya daga cikin ginshiƙan waƙoƙi, ta hanyar zuga ne ya kan kambama ya tsima shi ya kuma sa shi ya nuna jaruntaka da ƙarfin zuciya domin aikata wani abu na bajinta. An kawo ma'anar zuga da kuma wasu misalan zuga a cikin wasu waƙoƙinsa tare da sharhin zuga a cikin waƙoƙin Kassu daga ƙarshe an kawo kammalawa.

## 1.1 Taƙaitaccen Tarihin Kassu Zurmi

An haifi Alhaji Abubakar Kassu Zurmi a shekarar 1923, a garin magarya ta ƙasar Zurmi, kuma a ƙaramar hukumar Zurmi, a jihar Zamfara a yanzu. Makaɗin ya sami wannan suna ne na Kassu daga laƙabin *MaiKassuwa*, wanda aka gutsure ya koma "Kassu". Mahaifiyar sa ta haife shi ne a ranar kasuwar Dunfawa bayan ta dawo daga cin kasuwa.

Kassu ya gaji kiɗa ne a wajen mahaifinsa Muhammadu Ganga, wanda makaɗin farauta ne. Tun da Kassu Zurmi ya tasa, ya fara bin mahaifinsa yawon kiɗa da waƙa. Haka ya sa idon Kassu ya buɗe dangane da salo da dabarun kiɗa da waƙa da kuma sanin wasu 'yantauri da mafarauta. Bayan rasuwar mahaifinsa sai Kassu Zurmi ya gaje shi a fagen kiɗa da waƙa, musamman na mafarauta da 'yan tauri. Amma, shi Kassu ya shahara a fagen kiɗan farauta da na tauri da kuma kiɗan barayi ta hanyar amfani da kayan kiɗa na kalangu. A sakamakon shaharar Kassu, Sarki Zurmi ya naɗa shi Sarkin makaɗan maza na ƙasar Zurmi. Bayan kiɗa da waƙa kuma, Kassu yana taɓa noma. Kassu yana da kyakkyawar alaƙa da makaɗan baka na Hausa a zamanin rayuwarsa. Hakan ya sa Alhaji (Dr.) Mamman Shata Katsina yay biya masa kujera aikin hajji, wanda ya je ya sauke farali. Haka kuma, Kassu Zurmi ya na da abokan aiki guda uku waɗanda suke yi masa kiɗan kalangu, amma a tsari na rera waƙa, Makaɗa Kassu Zurmi makaɗin kaɗaita ne, wato shi kaɗai yake rera waƙoƙinsa ba a yi masa amshi. Allah ya yi wa Kassu Zurmi rasuwa a shekarar 1987. (Gusau, 2011:225-229 da Magaji, 2016:9-12 ).

## 1.1 Ma'anar Zuga

Ma'anarta ta harshe tana nufin hurawa. Idan an ce zuga ana nufin rura ko hura ko harguɗa mutum ko kumbura shi. Ana iya yin wannan harzuƙawar ta hanyar waƙa ko kirari, ko kuma ta hanyar magana irin ta yau da kullum. Ita wannan harzuƙawar ana yinta ne domin ingiza mutum ya yi wani abu ko ya ƙi aikatawa, ko kuma ya ji shi a cikin ransa.(Dunfawa 2004).

Zuga wata magana ce da ke ɗauke da wasu kalmomi da ake amfani da su a koɗa wani a cicciɓa shi a nuna fifikonsa kan wasu (Gusau, 2002:302). Zuga ta ƙunshi sashen waƙa wanda ke ƙoƙarin ya sosa zuciyar Basarake har ta kai ga sa shi jin ya fi kowa kuma mai iya aikata komai ya ga dama ne ba tare da samun wani mai tare shi ba. Jigo ne wanda kalmominsa ke kambama basarake su ciccika shi su ingiza shi ga yin abubuwan da in babu waƙar da wata ƙila ba zai yi matakin aikata su ba (Yahya, 1997:131).

Zuga ta ƙunshi waɗansu kalmomi da akan faɗa wa mutum domin ƙara masa ƙarfin zuciyar yin wani abu wato harzuƙa ko tunzura wani (CNHN, 2006:495). Dangane da maza zugar da akan yi musu yawanci domin su aikata ɓarna ne. Wato zugar da ake yi wa maza kamar tura mai kantu ruwa ne.

Zuga tana ɗaya daga cikin muhimman abubuwan da ya cancanta waƙoƙin maza su ƙunsa. Dalili kuwa shi ne, ta hanyar zuga ne za su sami ƙarfin zuciyar yin wasu abubuwan jaruntaka da za su nuna su maza ne. Dangane da wannan kuwa kusan Kassu Zurmi ya zarce kowa. Ana ganin zai fi ma'ana idan aka nuna yadda zuga take a kowane rabo na waƙoƙin 'Kassu Zurmi. Da farko za a duba zuga a waƙoƙin 'yan tauri. Su dai 'yan tauri suna harkokinsu ne a gida ba a daji ba, domin dukkan ɗan tauri da ya fita daji ya zama ɗan farauta. Lokacin da Kassu ya ziyarci gidajen 'yan tauri, sannan ne yake yi masu kiɗa har su tsima su yi kiraye-kiraye, wanda kan kai ga zage-zage. To, irin wannan idan wani ya rama, shi kai ga faɗace-faɗace. (Magaji, 2016:26).

## 1.2 Waƙar Na Gidan Mamman Abin Tsoro

Ya dai saba da 'yan doka
Ya dai saba da 'yan doka
Yanzu ha Alƙali ba ya nuni nai
Sai dai ya yi mai jawabi
In yas swaka mai ya swaka mai

A nan Kassu ya zuga Mamman ya tursa shi yana ce masa ya fi ƙarfin 'yan doka wato ya fi ƙarfin a hukunta shi.Kassu ya zuga Mamman yana nuna mishi, shi babban mutun ne ya fi ƙarfin kowace hukuma balle ma hukuncin da za a yi mishi.

**1.3. Waƙar Mai Shibra**

Iro ya kan bugi ƙato guda ya hwaɗi talatin
Kowace kau hwaɗuwa da mullen kashi
Wa kaj ji yana biɗa Iro na Labbo
Ɗan gida ko baƙo,yanzu a amso rainai
A kai Hakimmainai

Kassu ya zuga Iro a wurin dambe da cewa in ya bugi ƙato guda sau talatin ƙaton ke faɗuwa, a nan Kassu ya yi ƙoƙarin zuga Iro ya nuna masa yana da ƙarfi da bajinta da kuma buwaya. Anan Kassu na zuga shi watau in ya bugi ƙato bayan ya fadI sai ya yi ƙiran kashi saboda zafin bugun . Bugu guda sai ya yi mulmula talatin saboda zafin bugun da an ka yi mai.

**1.4 Waƙar Mai Shibra**

Daɗa Maishibra ya ci mugun tauri
Ga aya nan tana hita ga jikinai
Kuma yana da makamai
Dauri ba kamar yau ce ba.

Kassu ya zuga Maishibra yana nuna ya ci mugun tauri don haka ya buwayi kowa saboda yana da manyan makamai waɗanda za su sa kowa ya ji tsoron sa ya buwayi kowa wane mutun ya buga da shi.

**1.5 Waƙar Shallo**

Ka ji na Bello ya ƙananen ba
Bari dai a ba ku rancen tsaba
Ku mayad da Soshiya don gayya
Na Jibiri nasara ko ta ci ƙasag ga
Iro hay yau ba a ima Gobirawa ga hwaɗa ba
Azara'ila maganin wanda ka sheɗa
Iro ina jikan Geshe maganin matsoraci.

Kassu ya zuga Bello har inda ya danganta shi da Azara'ilu ya zuga shi wato ba tsoro saboda ya san Azara'ilu ɗibar rai yakai, haka shi ma Bello in ya yi faɗa da mutun kashewa ya kai. Shi Bello maganin matsorata ne babu wanda yake tsoro haka yaka ɗibar rayuwa ya gagari mutane, nan take kashewa ya kai, ba ruwansa da wasa.

**1.6 Waƙar Nomau**

Baba in sata ka kai yi sata ka saye
In kau ka ga ba ka sata yi hwashe
Amma na baz zuwa gida ba ni da shi
Baba kunya naka ji
Abdu jikan Jatau baba maƙi gudu

Karen masu gari.

A nan Kassu na zuga Nomau da ya yi sata ko fashi don a sayi dokin da aka yi masa alƙawali.Kassu ya zuga shi kar ya fasa alƙawalin sayen doki duk abinda zai yi, ya yi don ya sayi doki ko da sat a ce in ji Kassu.

Haka kuma a waƙar ta Nomau ya sake cewa:

Lahani mai ta da ciniki ba a saye
Kanƙan dambe maganin masu kwaɗai
Dokin na baz zuwa gida ba ka yi shi ba
Yaz zo yac ce Saraki ka gas shi
Doki sabad da shi za ni hwashe.

Kassu ya zuga shi kuma ya aminta da shi, ya yi amfani da zugar ya ta da hankalin masu gari har ana ƙoƙarin haɗa masa kuɗin doki.

Bari in ba ka shawara
In kab bi ta gobe dokin aka yi
Magarya ko ba a da shi
Allah dai ya kai mu gobe da swahe
Karhe bakwai na swahiya
Sai iskan nan ya taso wanga
Na ibag gujiya mai kwasas Sansami
Yana gamawa da ƙasa
Ya bar hwaka kar kar kar
Sai ka ji dattiɓai na gungu-gungu
Suna Allah Shi raba mu da iskan ga lahiya.

Ya zuga Nomau da cewa ya bari sai lokacin iskan hunturu ya tafi ya banka wuta ga garin daga gabas, tun da sun ƙi ba da dokin da girma da arziki.

Kassu ya ci gaba da zuga Nomau ta hanyar da zai bi har a samu doki, da ya yi sata. Kassu ya yi sati yana zuga Nomau ya san kowace irin hanya zai bi domin ya samu doki, ya ƙara da cewa:

Sannan ebo wuta ga ragga ka hita
Ba dai mai gini Magarya sai na rihewa
Koma daz zuwa gidan ɗan Aljanu
Banka 'yab bura uba sai daji na Magarya
Rantsuwa kattta kasai.

Ya ƙara da cewa:

Wuta nah hissan bilal kauta
Yac ce Kassu shawarakka ita za ni biya
Baba in kan ka bi ta
Gobe dokin aka yi
Magarya ko ba a da shi
Sai ga Nomau ana ta gyaran kulki
Da kambuna za a hwashe
Ihim.

Kassu ya zuga Nomau, yana ta gyaran kulkin sa wanda za shi da sauran kayanshi kuma ya yarda da zugan ya aikata abin da Kassu yake son ya yi.

Ina biye ni kau ina yi mai mabanci
Ina hwaɗin in dai ba a sonka
Tungag ga hita.

Kassu yana biye da shi yana zuga shi cewa tun da ba a son shi garin ya fita amma ba fitar alheri ba. Ya yi duk abinda ya ga dama, ya cinna wabgarin wuta lokacin da wutar za ta yi mummunan tasiri ga garin.

### 1.7 Waƙar Kwazo Sabattacce

Nic ce mai ƙwazo subattacce
Sabattacce
Sai ya watce itace nai
In ba Wanakiri ya ɗau rai ba
|arawo mai rai guda ya yi gida
Da abi nai.

Kassu ya nanu ko da ya ƙwazo ya mutu, an binne shi, idan ya tafi bakin kabarin Kwazo, idan ya yi masa kirari to Kwazo zai zubar da itacen kabarinsa ya fito daga kushewa, idan dai wanakiri bai sake ɗaukar ransa ba. Wannan ya nuna mana irin tasirin kiɗa da kirarin Kassu ga 'yan taurin nan.

### 1.8 Waƙar Mani

A cikin waƙar Kassu ya kawo zuga kamar haka:

In ba maganab banza ba
Mani bai yi idon tsoro ba
Ko kusa ba shi da tsoro kowa
Kowon nune shi yana sara nai.

Inda Kassu ya zuga Mani da cewa ai maganar banza ce, ba ya tsoron kowa ya nuna masa ya fi ƙarfin kowa, kuma kowa ja shi ya sare shi ko ya kashe shi, ba a komi dan ya is aba mai iya ja da shi saboda jaruntakar shi da bajinta.

### 1.9 Waƙar Auta Baban Suri

Bahago na Sambo kad da ka hwasa bugu sa rai ya ƙore
Kahin dangin mutum su zo
Su iske agullai na ci mai kai.

A nan Kassu ya zuga Auta ya nuna masa cewa ya buge shi har sai ya mutu ko kafin 'ya uwansa su zo sai dai su iska gawarsa kuma ba a komai don ka isa.A nan Kassu ya zuga auta ya nuna ya fi ƙarfin kowa.

### 10 Waƙar Ɗan Sale

Albishirinka Ɗan Sale ga jan banza
Ka da ka hwasa su sai ka bari sun dawo
An dawo dag Gusau an game ma Kuɗɗi .

Kassu ya zuga Ɗan sale da ya je ya yi fashi ya samu kuɗi ya je ga 'yan kasuwa da suka dawo daga Gusau ya samo don ya ba su kasonsu don shi ba shi nashi kaso. Ya umurce shi da kada ya yi saurin zuwa gidajen fataken, a'a ya bari sai sun dawo daga cin kasuwa, sun haɗa kuɗaɗen sannan ya tafi ya yi musu sata.

.

**Kammalawa**

Kassu kasancewarsa shahararren mawaƙi wanda yake amfani da salallai daban-daban a cikin waƙarsa, kamar yadda muka gani a wannan muƙala inda yake zuga waɗanda yake ma waƙa domin ya kambaɗa su ya tsima su domin su aikata wani abu da yake son su aikata. An yi nazarin waƙoƙin Kassu guda tara aka fiddo da zuga a cikin waƙarsa.

**Manazarta**


Dunfawa, (2004) Zuga a Cikin Waƙoƙin Fada. *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies*. Department of Nigerian Languages Series IV, Benchmark Publishers Limited No. 29 AK Business Complex Aminu Kano Way, Goron Dutse Kano, Nigeria.

Gusau S.M.(2002).'Salihu JankidI Sarkin Taushi. Kaduna; Baraka Press and Publishing Limited.

Magaji, A. (2016). Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa, Spectrum Book Limited Ibadan. Spectrum House Road.

Kamusun Hausa (2006). Na Jami'ar Bayero Kano.

Yahya A B, (1997). *Jigon Nazarin Waƙa,* FISBAS, Kaduna.

Zurmi M.A, (1986).' Rayuwar Alhaji Kassu Zurmi Da Waƙoƙinsa' Kundin B. A Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo, sokoto.